# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na goma sha huɗu: Hanyar lafiya – a bi ta da shekara

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Lami: | 'yar shekara 20 |
| Matar M. Talle: | 'yar shekara 55 |
| Magaji: | ɗan shekara 22 |
| Ralph: | ɗan shekara 40 |
| Roda: | 'yar shekara 19 |
| Faisal: | ɗan shekara 19 |
| Jami'in shige da fice: | ɗan shekara 40 |

**Mai gabatarwa:**

Jama'a, barkanmu da sake saduwa a cikin shirin "Ji Ka Karu". A yau mun shiga kashi na goma sha huɗu daga cikin jerin wasan kwaikwayon da muke kawo muku ta wannan gidan rediyo mai taken "Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai", wanda a cikinsa muke duba abubuwan da suke jan hankalin 'yan Afirka suke yin ƙaura zuwa Turai, da kuma irin halin da suke shiga.

Sai ku gyara zama ku ji yadda za ta kasance a wannan shiri namu mai suna "Hanyar lafiya – A bi ta da shekara". Bari mu fara da Lami wadda take yin waya a ruɗe.

**Fitowa ta 1: Lami ta kira babarta ta wayar salularta**

**Lami:** Amsar wayar nan mana, Mama, amsa! Don Allah ki ɗaga wayar nan!

**Matar M. Talle:** Alo? … Me ya yi zafi haka Lami? Kiran waya da tsakar dare haka.

**Lami:** Mama… Ina… na...

**Matar M. Talle:** Kina me?! Lafiya kuwa, Lami? Me ya faru haka? Me ke faruwa ne?

**Lami:** Wallahi ba zan iya ba, Mama, so nake na dawo gida! Ni gida nake so.

**Matar M. Talle:** Kin ga saurara, Lami! In dai don jikin babanki ne, ki kwantar da hankalinki! Likitoci sun tabbatar mana da cewa yana murmurewa, tun da an yi masa aikin. Don haka ba wani abin damuwa ba ne. Kuma kin san ba don ke ba, to da ba a yi masa wannan aikin ba.

**Lami:** Mama, na yi murna da jin cewa Baba yana samun sauƙi. Amma wannan ba shi ba ne yake damuna.

**Matar M. Talle:** To ke kuwa mene ne ya faru haka? Na san dai ba kewar gida kike yi ba don kuwa ba ki daɗe da komawa ba. Kuma na ga abubuwa na gara miki a nan Turai.

**Lami:** Don Allah Mama, ki yi haƙuri, na dame ki cikin dare! Don Allah ki yafe min duk abin da na yi!

**Matar M. Talle:** Haba Lami, ke kuwa me kika yi? Faɗa min duk abin da ke damunki! Ni babarki ce. Ko ma mene ne, ko da juna biyu ne, akwai yadda za mu yi mu samu mafita! Kada ki yi gaggawar ɗaukar matakin abin da bai dace ba.

**Lami:** A'a, ba ni da juna biyu. Mama, yi haƙuri, ba zan iya yi miki bayanin abin ta waya ba! Zan dakata haka. Sai da safe. Ki ce da Baba ya yafe mini!

**Matar M. Talle:** Saurara Lami! Lami, ki saurara!...

**Mai ba da labari:**

Yanzu kuma bari mu ji abin da ya faru ga Magaji. Bayan da ya tsere daga sansanin ajiye 'yan gudun hijira ya haɗu da Roda a hanya wadda ta yi alƙawarin taimaka masa. Amma bayan ya bar gidanta, Magaji ya rasa yadda zai yi, kuma ya rasa inda za shi. Ba shi da ko kwabo, don haka sai ya faɗa rayuwa marar daɗi, yana kwana tare da sauran mutane marasa galihu waɗanda suke kwana a tashar jirgin ƙasa, ko a tituna, ko a farfajiyar wuraren shaƙatawa. Wani daga cikin mutane marasa galihu ne ya taimaka masa, ya sami aikin kula da shukoki ba bisa ƙa'ida ba wanda ake biyansa a hannu. Magaji yana yi wa wani mutum ne mai suna Ralph aiki, wanda ya yarda zai

dinga biyansa duk ƙarshen sati. Bari mu ji irin wainar da yake toyawa yayin da yake aikin.

**Fitowa ta 2: Magaji yana aiki a matsayin mai kula da shukoki**

**Ralph:** Kai! Kai! Me kake yi haka? Na faɗa maka kada ka datse shukokin su yi ƙasa da yawa. Yanzu dubi ɓarnar da ka yi min. Dukkanin maƙwabta da masu wucewa na ganin cikin ɗakunana.

**Magaji:** Amma Yallaɓai, ina datsewa kamar yadda ka gwada min. Ba daɗi ba ragi.

**Ralph:** Me ka ce? Wato kana so ka faɗa min cewa ban ma san abin da nake faɗa maka ba? Ku dai 'yan Afirka haka kuke, ba kwa fahimtar komai. To ai shi ke nan, ba zan biya ka ba, tun da ka lalata min shingena gaba ɗaya.

**Magaji:** Yaya za ka yi min haka? Yau sati guda ke nan ina aikin awa goma kullum a lambunka! Duk abin da ka sa ni shi nake yi. Ya kamata ka biya ni ladana kamar yadda muka yi ƙa'ida.

**Ralph:** Wato ma yanzu wata barazana kake yi min ko? Wace ƙa'ida kake magana ne ma tukuna? Ban san inda maganarka ta sa gaba ba. Ban taɓa sa hannu a wata yarjejeniya ba. In ka ci gaba da matsa min cewa sai na biya ka a kan ka ɓata min shingena, to zan fada wa 'yan sanda kana aiki a nan ba bisa ƙa'ida ba.

**Magaji:** Ka ga, na tsaya na yi maka aiki tuƙuru har na tsawon sati guda, Mista Ralph. Na cancanci ka biya ni.

**Ralph:** To ai sai ka yi ta yi! Ni kuma zan kira ’yan sanda, za kuma a mayar da kai Afirka! Na gaya maka!

**Magaji:** Allah, sai na yi maganinka!

**Ralph:** Me kake nufi? Kai, ajiye injin nan! ... Jama’a, ku taimaka, ku taimaka!...

**Mai ba da labari:**
Allah dai ya sa Magaji ya danne zuciyarsa. Shi kansa ya yi mamakin abin da ya aikata. Shin me ya same shi ne? Irin wahalhalun da ya shiga tun lokacin da ya yanke shawarar tsallakawa zuwa Turai sun fara tasiri a kansa. Nan da nan sai Magaji ya ranta a na kare, sai ga shi a ƙofar gidan Roda a ruɗe, ya dage ƙarfinsa yana ta danna ƙararrawa.

**Fitowa ta 3: Magaji a gidan Roda**

**Roda:** Wane ne haka yake ta danna min ƙararrawa?

**Magaji:** Roda, ni ne Magaji. Don Allah buɗe min!

**Roda:** Magaji! Me ya faru haka? Sai ka ce wanda aka koro?

**Magaji:** Kai Roda! Na kusa yi wani ɗanyen aiki. Ni kaina a firgice nake. Guduwa na yi, kuma ban san inda kai kaina ba.

**Roda:** In ce ko dai lafiya? Ko dai wani abu ne ya faru?

**Magaji:** Yau sati guda ke nan nake wa mutumin nan aiki, amma sai ya ƙi biya na. Raina ya yi matuƙar ɓaci, har na yi masa barazana, ko da yake ban dai taɓa shi.

**Roda:** Ina ganin ya kamata ka ɗan ba ni labarinka, Magaji, saboda lokacin da na taimaka maka kwanan baya na fahimci ba ka so na san ko kai wane ne. Ba ni labarinka! Guduwa ka yi? Ko wani laifi ka yi? Ko ka shigo Turai ne ta haramtacciyar hanya?

**Magaji:** Gaskiya ne. Na shigo Turai ne daga Afirka ɓoye a cikin wani jirgin ruwan ɗaukar kaya. Su ne suka ce za su mayar da ni, ni kuma sai na gudu.

**Roda:** To amma a kan me? Me ya sa ka yi irin wannan kasada haka, ka sai da ranka, ka zo kake garari a titi? Wannan yana ɗaure min kai wallahi, Magaji.

**Magaji:** Me kike nufi? Ai haka kowa yake yi. Ke ta yaya kika shigo Turai? Ko a nan aka haife ki?

**Roda:** A'a, ba a nan aka haife ni ba. Na zo ne a matsayin mai ronon jarirai. Bayan na gama karatun sakandare, sai na yi rijista da wani kamfanin sama wa ɗalibai renon jarirai, bayan 'yan kwanaki sai suka sama min aiki a Turai.

**Magaji:** Ki bari don Allah? Kina nufin ni ma da na bi wannan hanyar da ban shiga wannan tashin hankalin da na shiga kafin na zo nan ba?

**Roda:** E to, ba na jin irin waɗannan kamfanonin suna ɗaukar maza aiki, amma na san akwai wasu kamfanonin da suke harkar wasu ayyukan, musamman idan kana da takardar shaidar karatun wata sana'a. Amma duk da haka, ni dai na yi sa'a saboda waɗanda suka ɗauke ni aiki suna da kirki. Sun ɗauke ni kamar 'yarsu, har ma shawara suka ba ni da

na ci gaba da karatu a nan. Zamana da su ya taimaka min wajen jin Turancina wanda hakan ya sa na sami sauƙin cuɗanya da mutane, na kuma yi ƙawaye da dama, har ma daga ƙarshe na sami shiga jami'a.

**Magaji:** Kai! Amma kin yi sa'a. Da na san haka abin yake ai da na faɗa wa Lami.

**Roda:** Magaji, wace ce kuma Lami? 'Yar'uwarka ce?

**Magaji:** A'a. Share kawai, ci gaba da bayani!

**Roda:** Bayan na kamala karatun digirina sai na sami aiki a matsayin mai ba da magani, na kuma sami takardar izinin yin aiki. Tun daga sannan nake zaune a nan, nake kuma taimaka wa 'yan'uwana a can gida.

**Magaji:** Amma abin gwanin ban sha'awa. Kina tunanin komawa gida kuwa? Na ga kin sami gindin zama a nan, amma dai ba ki da aure ko?

**Roda:** A'a, ba ni da aure, amma an sa mini rana, wanda kuma zan aura a Afirka yake da zama, a can kuma yake aiki. A ƙarshen wannan shekarar ma za a yi bikinmu. Daga nan kuma sai mu yi shawarar inda za mu ci gaba da zama.

**Magaji:** A gaskiya Roda na yaba da duk irin taimakon da kika yi min. Kin taimaka min sosai! Sai dai don Allah bari na roƙe ki wani muhimmin abu mana. Kin ga sati guda ke nan nake yi wa wannan mutumin aiki a lambunsa don na sami kuɗin tikitin zuwa cikin gari, amma kuma ya ƙi biyana, ga shi ba ni da ko kwabo. Ko za ki iya taimaka min da wasu 'yan kuɗi? Na san wani nauyi zan ɗora miki, amma ina matuƙar

son isa cikin gari. Ina so ne na isa jami'a.

**Roda:** Me zai hana? Nakan haɗu da mutanen da suke tambayata kuɗi da dama, amma na fahimci taka buƙata ta gaske ce Magaji. Haka kuma na fahimci kai mutumin kirki ne. Ban san me ya sa ka sai da ranka ka taho nan ba, amma na san dai wani muhimmin abu ne. ... Ga Yuro ɗari. Wannan zai ishe ka zuwa duk inda za ka. Ga kuma katina. Idan kana buƙatar wani bu ka iya kira na.

**Magaji:** Kai, na gode ƙwarai da gaske! Ban san ma irin godiyar da zan yi miki ba. Wallahi, na gode, Allah Ya saka da alheri!

**Mai ba da labari:**
.A can kuma wurin da ake tsare da baƙin haure an yanke hukunci game da neman mafakar da Faisal ya yi.

**Fitowa ta 4: An ba wa Faisal mafaka**

**Jami'in shige da fice:** Albishirinka, Faisal! Bayan kyakkyawan nazarin takardunka na neman mafaka da Hukumar Shige Da Fice ta yi, alƙali ya yanke hukuncin cewa ya kamata a ba ka mafakar. Ga kuma waɗannan takardun, su suke nuna cewa lallai kai ɗan gudun hijira ne mai 'yanci a wannan ƙasar. Yaya kake ji, Faisal?

**Faisal:** Kai! Amma na ji daɗi ƙwarai da gaske wallahi. Kai, na gode ƙwarai da gaske! Wannan muhimmin abu ne a wurina. Zan iya fara aiki yanzu?

**Jami'i:** Da saura dai, ɗan samari. Wannan shi ne mataki na farko.

Bari in yi maka ƙarin bayani yadda ƙa'idojin da 'yan gudun hijira suke bi a ƙasar nan. Za a kai ka sansanin 'yan gudun hijira inda za ka zauna. Ba za ka bar wannan wurin ba. Dole ne kuma za ka bi dokokin wannan sansanin. Hukuma za ta ba ka abinci, da wurin zama, da kuma 'yan kuɗi na kashewa. A iya ba ka kuɗi ko takardu waɗanda da za ka iya amfani da su wajen sayayya a wasu kantuna da aka ware. Ba ka da ikon yin wani aiki da za a biya ka ko a ina ne a matsayinka na ɗan gudun hijira. In ko ka nemi zin haka, to ya ka rasa mafakar taka. Ka fahimce ni ko?

**Faisal:** Umh… umh… Don Allah ban fahimce ka ba, ko za ka maimaita abin da ka faɗa? Ban fahimce ka sosai ba…

**Mai gabatarwa:**

To, da wannan hali da Faisal ya shiga na ruɗani da rashin tabbas a kan rayuwar 'yan gudun hijira a Turai muka zo ƙarshen kashi na goma sha huɗu.

Me za ku ce game da irin waɗannan dokokin da ake sa wa 'yan gudun hijira a Turai? Shin sun dace kuwa? Muna maraba da ra'ayoyinku ta shafinmu na Facebook, wato facebook.com/dw.lbe, inda za ku iya ba mu labarin 'yan Afirka da suka shiga Turai ta hanyar da ta kamata, suka ci ribar zaman nasu a can.